# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsakanin al'umma a Afirka
## Kashi na uku: Me ya faru yanzu?


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Fati: | 'yar shekara 16 |
| Gambo: | ɗan shekara 18 |
| Dauda: | ɗan shekara 40 |
| Hadiza: | 'yar shekara 30 |
| Julie: | 'yar shekara 40 |
| Tanko: | ɗan shekara 45 |
| Ɗan jarida | |
| 'Yar jarida | |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan cin zarafi da ya addabi ƙasashen nahiyar Afirka. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda 'yan ta'adda suka wulaƙanta Hadiza mai ɗakin Dauda, da kuma yadda ya fita nemanta a bakin kogi. Sannan shi kuma Adams, ɗan Precious, ya sha kashi a hannun manemin mahaifiyarshi, wato Jammo, a lokacin da ta bar shi Adams ɗin don ya kula da shi. Sai kuma makarantar kwana ta maza da mata in da Fati ta fara karatu, mamaki ya kama ta bayan irin maganganun da malam Tanko, mai kula da ɗakin kwana a makarantar, ya gaya mata. Ya ba ta sabuwar katifa amma kuma ya ce kar ta faɗa wa kowa. Wace manufa malam Tanko yake da ita? Sai ku kasance da mu domin jin abubuwan da za su biyo baya a wannan kashi na uku na wannan shiri.

Yanzu za mu faro ne daga inda Fati ta fita tana zagaya filin makarantar da gudu saboda sha'awar da take da shi na gudu. A lokacin ne kuma ta haɗu da wani ɗalibi mai suna Gambo.

**Fitowa ta 1: A filin wasa na makaranta**

**Fati:** *One, two… one, two… one, two…* Ok, yanzu bari in zagaya filin nan sau goma.

**Gambo:** Ji mana, sannunki… Ke sabuwar zuwa ce wannan makarantar ko? Ban taɓa ganinki ba. … Sunana Gambo. Ni ne zakaran gudun wannan babbar makarantar garin nan. Tun ɗazu nake ganin yadda kike gudu kuma na ga kin iya sosai.

**Fati:** Malam, me kake nema da ni?

**Gambo:** Ni? Ai to… ba komai, ba wani abu ba ne. Ni dai ina ɗan tunanin…

| | |
|---|---|
| **Fati:** | To, ai shi ke nan, kana ɓata min yadda nake guduna kuma kana ɓata min lokaci. Sai an jima. |
| **Gambo:** | Wallahi, kin ba ni dariya. Kin san abin da kike faɗa kuwa? Kin san ko mata nawa ne suke so su samu matsayin da kika samu yanzu haka? |
| **Fati:** | To ai shi ke nan, na bar musu matsayin. |
| **Gambo:** | Ji mana! Ko sunanki fa ban sani ba. |
| **Fati:** | Ai ba sai ka san sunana ba. Ina ganin kana da sunayen wasu da yawa da za ka riƙa tunawa. |
| **Gambo:** | Mhm, shi ke nan, wai za ki yi min yanga ko?! Amma ki san cewa ni ma a shirye nake. Za mu ƙara haɗuwa. |

**Mai ba da labari:**
Fati yarinya ce kyakkyawa kuma tana da wayo. Kuma tana da sha'awar gudu sosai, amma ta san cewa ta zo makarantar nan ne ba don wasa ba sai don ta ci jarrabawarta. Saboda haka sai ta ci gaba da gudunta. Amma ba tare da ta sani ba, ashe bayan Gambo Malam Tanko ma yana kallonta ta tagarsa, yana ganin duk abin da take yi. To, bayan ya ga Fati tare da Gambo sai ya yi tunanin cewa ya kamata ya yi wani abu cikin hanzari. Amma kafin mu ji abin da zai yi, bari mu je bakin rafin nan inda yanzu dare ya riga ya yi, kuma ga Dauda can riƙe da fitila yana neman matarsa Hadiza.

**Fitowa ta 2: A rijiya**

**Dauda:** Hadiza! Hadiza! Hadi… A'a! Hadiza! Me zan gani haka? Me suka yi miki? Hadiza? Wayyo Allah! Buɗe idanuwanki! Hadiza, ni ne, Dauda, mijinki. Don Allah, abin ƙaunata, tashi! Allah Sarki! Buɗe idanuwanki!

**Hadiya:** Arrgh… Wasshhh! Arrgh… Uhmmmm...

**Dauda:** Hadiza! Kar ki damu! Kina da rai! Allah na gode maka. Na ji daɗi da na ji muryarki. Ba sai kin yi magana ba. Ina nan. Yanzun nan zan kai ki asibiti, kar ki damu, zan kula da ke sosai. Amma wallahi, duk wanda ya yi miki wannan abin, wallahi sai na nemo shi kuma sai na kashe shi! Sannu! Sannu Hadiza!

**Mai ba da labari:**

Yanayin da ya sami matarsa a ciki sai da ya sa Dauda ya ji kamar an daɓa mai wuƙa a zuciyarsa. Sai duk zargin kanshi da kanshi yake yi cikin fushi da ɓacin rai, amma sai ya danne zuciyarsa. Sannan bayan ya dawo cikin hankalinsa sosai sai ya kama matarshi, ya ɗaga ta tsaye da ƙafafuwanta, sannan ya rufe ta da ɗan ƙyallen da ya rage mata, sannan ya kai ta asibiti. Wanshekare sai jaridu suka fito da labaran yadda wata ƙungiyar 'yan ta'adda take bin wuri-wuri tana yi wa mata fyaɗe. Ɗaya daga cikin waɗanda labarun ya sosa wa zuciya, wata mace ce mai suna Julie. Julie tana aiki ne da wata ƙungiya mai zaman kanta, kuma mai yaƙi da cin zarafin 'ya'ya mata. Saboda haka daga jin abin da ya faru, sai ta kira taron 'yan jarida.

## Fitowa ta 3: A taron 'yan jarida

**Julie:** Jama'a, barkanmu da warhaka. Na gode ƙwarai da gaske da kuka samu amsa wannan gayyatar, duk da cewa an faɗa muku ne a ƙurraren lokaci. To, kamar yadda kuka ji, an

samu wasu ƙungiyar 'yan ta'adda ne suna bi wuri-wuri suna yi wa mata fyaɗe, suna cin zarafinsu, kuma suna wulaƙanta su. Wannan abu ya tayar mana da hankali ƙwarai da gaske, wanda hakan ya ƙara fito da cin zarafin da ake yi wa mata. Wannan ƙungiya tamu ta sha ba wa mata taimako a kan su miƙe don su yaƙi cin zarafin da ake yi musu.

**'Yar jarida:** Wannan gaskiya ne. To yanzu, Julie, wane hoɓasa ƙungiyar nan taki za ta yi ne a kan abubuwan da suke faruwa?

**Julie:** To, kamar yadda muka saba, babban ƙalubalen shi ne na mu faɗakar da waɗanda abin ya shafa ne a kan cewa akwai inda ake ba da taimako da kulawa ga waɗanda irin wannan abin ya shafa. Za mu taimake su wajen kai ƙara idan suna so. Kungiyarmu za ta iya ba su shawarwari dangane da shari'a da kuma kula da lafiyarsu.

**Ɗan jarida:** To, wane mataki kuke ɗauka a ƙungiyance na ganin cewa wannan yunƙuri naku ya isa ga jama'a?

**Julie:** E to, muna shirin gudanar da wata zanga-zangar lumana don mu yi Allah wadarai da wannan ɗabi'a ta dabbanci, kuma muna kira ga mata da maza gaba ɗaya da su ba mu goyon baya a kan wannan ƙuduri namu. Kuma muna buƙatar a gudanar da cikakken bincike a kan wannan aika-aika, sannan ba za mu yi ƙasa a gwiwa ba har sai an kamo waɗanda suke da hannu a wannan aika-aika. Na gode.

**Ɗan jarida:** To Madam Julie, yaushe za ku gudanar da wannan zanga-zangar lumana, kuma ina ne?

**Julie:** Ina sauri ne, amma idan lokaci ya yi za mu sanar da ku.

**Mai ba da labari:**

An kafa ƙungiyar Julie ne mai yaƙi da cin zarafin mata da nufin kare hakkin jama'ar da suka samu kansu a cin zarafi ta hanyoyi dabam-dabam, da kuma su taimaka wajen gudanar da bincike a kan batutuwa na fyaɗe, da kuma samar da taimako a kan gudanar da shari'a, da kuma ba da taimako don waɗanda abin ya shafa su samu lafiya kuma su ci gaba da rayuwarsu tare da taimakon kansu da kansu. Ɗaya daga cikin abubuwan da ke ba su wahala shi ne gudanar da tattaunawa da kuma kula da lafiyar waɗanda abin ya shafa. Yawanci waɗanda aka yi musu fyaɗe, ko kuma aka ci zarafinsu na shiga wani irin hali na rashin mantawa da abin da ya faru gare su.

Amma yanzu bari mu ƙara komawa makarantar su Fati inda darasinsu na ƙarshe a yau a kan halittar ɗan Adam ne, kuma wane ne malamin da zai koyar da su? Malam Tanko.

**Fitowa ta 4: A makarantar su Fati**

**Tanko:** A yi shiru, a yi shiru! Ya isa haka! A saurara! Darasinmu na yau za mu yi shi ne a kan yadda ake samun haihuwa. … A saurara! Hanyar da ake samun haihuwa shi ne ta saduwa tsakanin mace da namiji. Saboda haka 'yammata sai ku yi kaffa-kaffa saboda za ku iya samun juna biyu in ba ku yi a hankali ba. … A yi shiru mana! Sannan ku ma mazan sai ku yi hankali, saboda ba ku shirya zama iyaye ba tukuna. … Ni ban ga wani abin jin daɗi ba dangane da wannan maganar. Amma abin mamaki duk sanda nake koyar da wannan darasi sai in ga ana ta shewa. … To, shi ke nan. Sai ranar Litinin idan Allah ya kai mu. Waɗanda za su je gida *weekend*, ku gai da iyayenku. … Fati, don Allah ko za ki ɗan dakata, ina son gan ki.

**Fati:** To, Mallam Tanko.

**Tanko:** Ɗan rufe ƙofar nan. Surutu ya yi yawa. … Fati, kin zo makarantar nan ne don ki yi karatu ko kuwa don ki yi yawo da maza?

**Fati:** Malam? Me kake nufi?

**Tanko:** Kar ki mai da ni sakarai mana! Kin san cewa a matsayina na shugaban sashin ɗakunan kwana na makarantar nan, ni ne kuma na biyu a matsayi bayan *principal* ɗin makarantar nan. Saboda haka na san dukkanin abubuwan da suke faruwa a makarantar.

**Fati** Amma… Amma Malam, ni har yanzu ban san...

**Tanko:** Babu wani amma. Na gan ki a filin wasa tare da Gambo. Me kuke tattaunawa?

**Fati:** Ba wani abu! Yana so ne kawai in san cewa shi ne *champion* ɗin gudu na babbar makarantar garin nan. Ni kuma ban nuna sha'awa a kan in sani ba. Shi ke nan.

**Tanko:** Fati, in ni ne ke, zan yi hankali da wannan yaron sosai. Bayan haka ma ban gamsu da aikinki ba a *biology*. Kina yin ƙoƙari sosai a sauran ɗarussa. Amma ina ganin zan iya taimaka miki a wannan ɓangaren.

**Fati:** Malam Tanko, ina iyakacin ƙoƙarina. Don Allah ka yarda da ni.

**Tanko:** Na yarda da ke mana. Me ya sa kike ganin na ware ki ke ɗaya daga cikin sauran? Saurare ni ki ji, Fati. So fa nake ki fi kowa a ajin, kuma a shirye nake in taimake ki a kan

haka. Amma ke ma sai kin taimake ni.

**Fati:** A'a, Malam me kake yi haka? Don Allah, Malam ka ƙyale ni, Malam don Allah ka daina.

**Tanko:** Ni malaminki ne, Fati. Ba zan ba ki wahala ba. Ba zan yi miki kuma abin da zai cutar da ke ba. Ina so ne kawai in shirya ki don ki zama cikakkakiyar mace. Kina so ki ci *biology*?

**Fati:** Haba Malam…

**Mai gabatarwa:**

Fati ta shiga wani hali. Ta gane cewa malam Tanko yana ta taɓa ta ne, kuma ba ta san yadda za ta yi ta gudu ba. Ta rufe idanuwanta, sannan ta fara tunanin ga ta can a filin wasa tana gudu, tana ta zagaya fili da gudun tsiya, gudu mai tsawon gaske wanda ya ƙi ƙarewa. Bayan lokaci mai tsawo sai ta buɗe idanuwanta, sannan kuma sai ta gane cewa Malam Tanko ya riga ya tafi. Amma ta san cewa wani mummunan abu kuma na kunya ya faru gare ta. Rigarta a buɗe take. Me Fati za ta yi a kan wannan cin zarafin da malaminta ya yi mata? Za mu ji wannan labarin da ma ƙarin wasu a shiri na gaba.

Kuna iya lalubarmu ta adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe domin ƙara sauraron wannan shirin da ma wasu, ko kuma a shafinmu na Facebook. Sai mun sadu a shiri na gaba. A huta lafiya.